JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA 11 Jimada al- Ah-khir, 1443
MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI 14 Junairu, 2022

(١)

# KYAWAWAN ƊABI'UN ZAMANTAKEWA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Lallai Allah yana bayar da umurni yin aldalci, da kyautatawa, da bayar da sadaka ga makusanta, yana kuma hana aikata alfasha da abubuwan ƙi, yana yi maku wa'azi ne ko za ku wa'aztu)** [an- Nahli: 90], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai samun kafuwar kyawawan ɗabi'u, dalili ne da yake nuna ɗaukakar al'umma, da cigabanta, shi ne kuma sirrin haɗin kai, da zama tsintsiya maɗaurinki ɗaya, da kuma samun kwanciyar hankali a cikinta, haka ma rushewar al'umma da rayuwar zamantakewa yana farawa ne a daidai lokacin da tsarin kyawawan ɗabi'u ya fara rushewa, duk rayuwar zamantakewar da ba a gine ta akan kyawawan ɗabi'u ba, to tun ranar da aka fara ginata ne ta ɗauko sirrin rushewarta; saboda ta ginu ne akan harsashe mai matuƙar rauni, alhairin Allah ya kai wurin mawaƙin da yake cewa: **"Ba wani abu ne al'umma ba, da ya wuce kyawawan ɗabi'u, matuƙar suna nan, to al'umma ma tana nan, kuma da zaran ka ga al'umma ta wargaje, to kyawawan ɗabi'un ciki ne suka wargaje".**

Babu shakka addininmu mai daraja ya bai wa kyawawan ɗabi'un zamantakewa da suke kare rayuwar al'umma, su kuma ƙarfafi rukunnansa, muhimmanci matuƙa; saboda kiyaye kyawawan ɗabi'u shi ne tushen wannan addini mai girma,

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ai da ma an aiko ni ne saboda in cika kyawawan ɗabi'u).**

A cikin waɗannan kyawawan ɗabi'un akwai: ɗabi'ar taimakekeniya, da taimakon marasa shi, da kuma rayuwar tare, waɗanda amfaninsu yake dawo wa ɗaukacin al'umma, ita ƙasa ta ɗaukacin 'yan ƙasa ne, tana kuma miƙewa ne tare da irin ƙoƙari da hoɓɓasar da suke yi gaba ɗayansu, ba tare da bambanci na addini, ko launin fata, ko jinsi ba, ta haka ne ake kashe son kai, da fifita kai, da nafsi- nafsi, kuma da haka ne ake kafa tushen 'yan uwantaka ta mutuntaka, abin da zai kai zuwa ga haifar da haɗaɗɗiyar al'umma, wadda ta ginu akan soyayya da baiwa, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku yi taimakekeniya akan biyayya da tsoron Allah, kada ku kuskura ku haɗa kai wajen aikata zunubai da zalunci)** [al- Ma'ida: 2], haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar junansu, da jinƙan junansu, da tausayin junansu tamkar jiki ne da idan wata gaɓa ta cutu, duka sauran jikin zai kamu da rashin barci, da kuma zafin ciwo)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai idan ƙabilar Ash'arawa suka shiga cikin tsananin buƙata a wurin yaƙi, ko abin iyalansu ya yi ƙaranci a garin Madina, sukan tattara gaba ɗayan abin da suke da shi a wuri ɗaya, sannan su sake rabawa a tsakaninsu daidai wa daidai, lallai su nawa ne, ni ma nasu ne).**

A cikin kyawawan ɗabi'u na zamantakewa akwai: gwarzantaka, da mutunci, da sadaukar da kai, da fifita wani akan kai, abubuwan da suke ƙara haɗin kai tsakanin 'yan ƙasa da suke rayuwa ta zamantakewa a wuri ɗaya, suke kuma ƙara dasa soyayya, da ƙauna, da zama da fararen zukata tsakanin al'umma,

wannan ne abin da Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya yi nuni zuwa gare shi a lokacin da ya hana yi wa juna ƙiyayya, da hassada, da juya wa juna baya, a inda yake cewa: **(Kada ku yi wa junanku hassada, kada kuma ku taya kaya da tsada da niyyar yaudarar masu saye, kada ku ƙetaci juna, kada ku juya wa juna baya, kada ku yi tayi akan cinikin juna..)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya tsaya wajen biyan buƙatar ɗan uwansa, Allah zai tsaya masa wajen biyan buƙatarsa, duk wanda ya yaye wa Musulmi wani baƙin- ciki, Allah zai yaye masa baƙin- ciki daga cikin baƙin-cikin ranar alƙiyama, duk wanda ya suturta Musulmi, Allah zai suturta shi ranar alƙiyama)**.

A cikinsu ma akwai: bai wa masu buƙatu na musamman, da marayu, da masu rauni, da tsofaffi kulawa ta musamman, ganin cewa kyautatamasu, da ba su kulawa wani abu ne da addini ya wajabta, kishin ƙasa da mutuntaka suka sanya ya zama tilas, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk yake kai- koma saboda macen da ta rasa mijinta, da miskini daidai yake da mai jahadin ɗaukaka kalmar Allah, ko daidai yake da wanda ya yi azumi da rana, ya kuma yi ƙiyamulLaili a dukan dare)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Shin wai ma za a taimake ku, a kuma azurta ku ne, ba domin masu raunin cikinku ba?!)**, kaman yanda Musulunci yake kallon ayyukan da masu buƙatu na musamman suke yi a matsayin wani abu mai ma'ana wajen cigaban al'umma, suna kuma zama abin koyi ne ga wasunsu, shi ya sanya addini ya ba su dama na su taka rawar da ta dace su a cikin rayuwar zamantakewa, Sayyiduna Abdullahi Bn Ummu-Maktum (Allah ya ƙara yarda da shi) shi ne mai kira wa

Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) sallah, haka ma ba sau ɗaya ba yana miƙa masa ragamar jagorancin garin Madina, ya jagorance su a sallah, ya kuma kula da al'amurransu.

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

A cikin muhimman kyawawan ɗabi'un zamantakewa akwai: bincike, da neman gaskiyar game da labaran da ake yaɗawa kafin mutum ya fara yaɗa su, da maimaita su, lallai Shari'ar Musulunci ta muhimmanta wannan kyakkyawar ɗabi'a mai nagarta, ta yi gargaɗi game da yaɗa jita- jita, da masu yaɗata, ganin cewa yaɗa jita- jita yana nufin rusa al'umma ta cikin gida, da kuma yaɗa ɗebe ƙauna, da sanya mutane su cire – rai, da kuma sacce wa 'yan ƙasa gwiwa, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani, idan wani fãsiƙi ya ƙetare shari'ar Allah ya zo maku da kowane irin labari, to ku bincika ku tabbatar da gaskiyarsa; saboda kada ku cutar da wasu mutane –da ba ku san haƙiƙaninsu ba-, hakan sai ya sanya ku yi nadama akan abin da kuka aikata, kuna: ina ma ba mu aikata hakan ba, a lokacin da bayani ya bayyana cewa ba su da wani laifi)** [al- Hujrat: 6], haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai mutum ya isa maƙaryaci idan yana bayar da labarin duk abin da ya ji)**, shi mai hankali a koda yaushe yana tunani ne kafin ya yi magana, shi kuwa wawa yana magana ne ba tare da ya yi tunani ba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Wanda duk ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya faɗi alhairi, ko kuma ya yi shiru).**

Lallai muna matuƙar buƙatar mu yi riƙo da kyawawan ɗabi'un zamantakewa, muddin dai muna son haɗin kai tsakanin ɗaukacin al'umma.

**Ya Allah Ubangiji ka shiryatar da mu zuwa ga kyawawan ɗabi'u, waɗanda babu mai shiryatarwa zuwa gare su sai kai.**